# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Daga Mai Tsanantawa zuwa Mai Wa'azi


**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**



**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**






**Allah ya yi abubuwa masu yawa wa mutanensa a farawar ikkilisiya. Wani mutum, sunansa Filibus, yana cikin gaya wa mutane a babban taron birni game da Yesu.**

**Amma Allah ya aike shi zuwa hamada. Don mene ne?**


Allah ya sani cewa akwai mai tafiya a hamadan, mai mulkia karkashin Sarauniya Kandace na Itiyofia. Yana cikin tafiya koma gida kuma yana karanta wani Littafi na musamman. Ko za ka iya gwada ko wane Littafi ne?
3
Sa’ad da Filibus ya yi biyayya ga Allah,
Allah ya bi da shi zuwa ga mai mulki wanda yake karanta Kalmar Allah ba tare da ganewa abin da yake karanta ba. Ya gayace Filibus ya zo su yi tare.
4
“Mene ne ma’anar wannan?” mai mulki ya tambaye Filibus. Yayinda keken dokin yana gangarowa a hanyar hamada, sai Filibus ya bude bakinsa, ya fara daga maganar Allah, sa’an nan ya yi masa wa’azi game da Yesu.
5
Ba a jima ba sai wannan mai mulki daga Afirka ya ba da gaskiya ga sakon Littafin, cewa Yesu Kiristi shi ne Dan Allah. Da ganin ruwa, sai ya ce, “Mene ne zai hana ni a yi mini baftisma?”
6
Sai Filibus ya ce, “Idan ka ba da gaskiya da dukan zuciyarka, za a iya yi maka.” Sa’ad da mai mulkin ya amsa, “Na ba da gaskiya Yesu Kiristi shi ne Dan Allah,” sai Filibus ya dauke shi zuwa wurin ruwam ya kuma yi masa baftisma.
7
Yanzu sa’ad da suka fita daga ruwan, Ruhun Ubangiji ya dauki Filibus ya tafi da shi, haka mai mulki daga Afirka bai gan shi ba. Sai ya koma zuwa Itiyofia yana farin ciki!
8


Amma wadansu mutane suka ki jinin Kiristoci. Istifanus, daya daga abokan Filibus, an kashe shi ta wurin mutane masu fushi wadanda ba su so su ji magana game da Yesu ba.  Wani mutum mai suna Shawulu daga Tasus shi ne ya taimake su domin a kashe Istifanus.
Shawulu ya ki jinin duka Kiristoci.
9


Shawulu, yana nishin barazana da kisa a kan Kiristoci, ya tafi wurin Babban Firist ya karbi wasika mai ba shi izini da ‘yanci ya kama maza da mata masu bin Yesu.
10


Shawulu abin tausayi na Tasus! Bai sani cewa yayinda mutum yana tsananta mutanen Allah, ashe Ubangiji Yesu ne da Kansa yana tsananta ba. Amma kamar yaya?
11


Allah ya “kama” Shawulu!  Yayinda Shawulu yana a hanyan zuwa birnin Dimaskos, Allah ya haskaka babban haske daga Sama. Shawulu ya fadi kasa. Sai ya ji Murya.
12


“Wane ne kai, Ubangiji?”  Shawulu ya kira da karfi.  “Ni ne Yesu, wanda kake tsananta.”  Cikin rawar jiki da tsoro, Shawulu ya tambaya, “Ubangiji, mene ne kake so in yi?”  Sai Ubangiji ya ce masa, “Tashi ka tafi cikin birnin, kuma za a gaya maka abin da za ka yi.”
13


Mutanen da suke tare da Shawulu su ma suka ji Muryar, amma ba su ga wani ba.  Shawulu ya tashi daga kasa – sai ya tarar ba ya iya ganin wuri!  Sai suka jagorance shi zuwa cikin Dimaskos.
14

A cikin birnin, Shawulu ya zauna a wurin har kwanaki uku babu ganin wuri ko ya ci ko ya sha. Watakila ya yi amfani da zarafin yana addu'a ga Ubangiji Yesu wanda ya sadu da shi a hanyar zuwa Dimashkos.



15

Allah yana da kome a shirye. A Dimaskos akwai wani almajiri mai suna Ananiyas. Ubangiji ya aike shi ya taimake Shawulu. Ananiyas ya ji tsoro. Amma ya yi biyayya ga Allah. Sa'ad da ya sa hannu a bisan Shawulu, makantan ya bar shi. – sai Shawulu ya cika da Ruhu Mai Tsarki na Allah.



16

An yi wa Shawulu Baftisma. Sai ya ci abinci. Bayan da ya karba abinci, sai ya sami karfin jiki. Shawulu yana bukatan karfi. Yana da abu na musamman da zai yi.



17

Nan da nan Shawulu ya yi wa'azin Kiristi a cikin Wuraren Hidimar Allah, cewa Kiristi shi ne Dan Allah. Sai duka wadanda suka ji shi suka yi mamaki, suka ce, "Ba wannan ne wanda ya hallakar da Kiristoci ba?"



18



Sabobi abokan gabansa suka sa ido a kofar birnin don su kashe idan yana so ya bar birnin. Amma abokansa, Kiristoci, suka dauke shi da daddare suka saukar da shi ta bangon birnin a kato kwando. Daga lokacin zuwa gaba, Shawulu mai tsananta wa Kiristoci ya yi rayuwa cikin aminci a matsayin mai bin sabon Maigidansa, Ubangiji Yesu Kiristi.

19

Daga Mai Tsanantawa zuwa Mai Wa'azi

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Ayyukan Manzani 8-9

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

20



# KARSHE

58 60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**